# Surah 91: Al-Shams - سورة الشمس

بسم الله الرحمن الرحيم

[91:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

وَٱلشَّمْسِ وَضُحَىٰهَا ١

[91:1] Ina rantsuwa da rana da hantsinta.

وَٱلْقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ٢

[91:2] Da wata dake binta.

وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا ٣

[91:3] Da yini dake bayyanawa.

وَٱلَّيْلِ إِذَا يَغْشَىٰهَا ٤

[91:4] Da dare dake rufewa.

وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ٥

[91:5] Da sama da wanda Ya gina ta.

وَٱلْأَرْضِ وَمَا طَحَىٰهَا ٦

[91:6] Da qasa da wanda da Ya sanya ta jure wa.

وَنَفْسٍ وَمَا سَوَّىٰهَا ٧

[91:7] Da rai da wanda da Ya halitta ta.

فَأَلْهَمَهَا فُجُورَهَا وَتَقْوَىٰهَا ٨

[91:8] Sa'an nan ya nuna mata mumunar abu da abu mai kyau.

قَدۡ أَفۡلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ٩

[91:9] Wanda ya rabauta shi ne wanda ya tsarkake ta.

وَقَدۡ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا ١٠

[91:10] Mai fadiwa shi ne wanda ya yi sakaci.

كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِطَغۡوَىٰهَآ ١١

[91:11] Kafircin Samudawa ya sa suka qetare iyaka.

إِذِ ٱنۢبَعَثَ أَشۡقَىٰهَا ١٢

[91:12] Sun bi mafi lalacewa daga cikinsu.

فَقَالَ لَهُمۡ رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقۡيَٰهَا ١٣

[91:13] Manzon ***ALLAH*** ya gaya masu cewa, "Wannan raqumar ***ALLAH*** ne; ku bari ta sha ruwa."

فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا فَدَمۡدَمَ عَلَيۡهِمۡ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمۡ
فَسَوَّىٰهَا ١٤

[91:14] Sai suka qaryata shi, sa'an nan suka soke ta. Saboda haka ne Ubangijinsu Ya darkake su, saboda zunubinsu.Ya halaka su.

وَلَا يَخَافُ عُقۡبَٰهَا ١٥

[91:15] Duk da haka, wadanda suka zo daga baya ba su tsoron irin aqibarta.